# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Almara a Afirka domin al'adu da zaman lafiya:
## Bari na ba ku labari
## Na goma: Biri da Kunkuru

| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Ibrahima Ndiaye |
| Waɗanda suka tace: | Yann Durand, Stefanie Duckstein, Naïma Guira |
| Wanda ya fassara: | Ɗanlami Bala Gwammaja |

**'Yan wasa:**

Mai ba da labari

Kunkuru

Biri

Giwa

Malam-buɗa-mana-littafi

MAI GABATARWA:

Masu sauraronmu, lale marhabin da sake kasancewa da ku a shirinmu na “Ji Ka Karu”. Wannan shi ne kashi na goma kuma na ƙarshe a cikin jerin hikayoyin da muke kawo muku na ƙasashen Afirka da ke koya zamantakewa tsakanin al’umma. A yau za mu ji yadda faɗa ya ɓarke tsakanin wasu dabbobi dabam-dabam guda biyu. Ɗaya daga cikin waɗannan dabbobin dai ya cika tsiwa, shi kuwa ɗayan mai ƙwazo ne. Yanzu sai ku gyara zama domin sauraron hikayar “Biri Da Kunkuru”.

MAI BA DA LABARI:

A wata shekara a gandun dabbobi an samu damina mai albarka, kuma kowa na sa ran amfani zai yi yawa kusan fiye da yadda aka saba gani. To, Kunkuru na daga cikin waɗanda suke yin noma tuƙuru, don haka ya sami amfani mai yawa. Ya samu gurji da abarba da kuma dankalin Turawa. Sai dai kuma duk da wannan bai gode ba.

KUNKURU:

“Kai, ina ma dai a ce har da masara na samu! Da dai a ce an ɗan surka min, ai da ba haka ba. Yanzu dole sai na ɗebi amfanina na kai kasuwa don a musanya min da masara.”

MAI BA DA LABARI:

To yanzu dai ga Kunkuru yana ɗauke da kwando a bayansa, yana tafiya da ƙyar cikin zafin rana. Can sai ƙarar tafiyar ruwa daga wata ƙorama da ke gefen hanya ta ja hankalinsa.
Sai ya ji ai ba zai iya wucewa haka kawai ba. Don haka sai ya ajiye kwandonsa a gefen hanya, ya lallaɓa ta cikin ciyayi har wajen ƙoramar don ya kashe ƙishinsa. Amma ko kun san wane ne yake wucewa a daidai lokacin da Kunkuru yake ajiye kwandonsa kuwa? Ai ba wani ba ne illa Biri.

BIRI:

"Hihihihi. Kai! Allah na gode maka, lalle na taki sa'a!"

MAI BA DA LABARI:

To Biri dai yana ta tafa hannunsa don murna saboda ganin wannan kwandon da ya tsinta a hanya. Nan da nan sai ya sace wannan kwando, ya haye saman wata bishiya don ya more wannan ganima da ya samu.
Yayin da Kunkuru ya dawo daga ƙoramar nan, sai abin ya zama kamar mafarki, don kuwa kwandonsa ya ɓace ko sama ko ƙasa. Nan da nan sai ransa ya ɓaci.

KUNKURU:

"A'a! Kai! Abin dai da ban mamaki! Sam, haka ba za ta saɓu ba! Yanzu-yanzu fa kwandona yake nan, amma yanzu na neme shi na rasa. Gaskiya wannan abin takaici ne. Kuma ni ga shi ban ga kowa ba wanda zan ce shi ya sace shi! To ai ba kome, ni dai na san ba mafarki nake yi ba!"

MAI BA DA LABARI:

Can sai ga Malam-buɗa-mana-littafi ya zo wanda a gabansa duk abin ya faru.

KUNKURU:

"Yauwa, Malam-buɗa-mana-littafi, don Allah ba ka ga wanda ya ɗauke min kwandona ba?"

MALAM-BUƊA-MANA-LITTAFI:

"Ɗaga kanka sama mana ka gani!"

MAI BA DA LABARI:

Sai Kunkuru ya ɗaga kansa sama ya kalli bishiya, sai ya ga kamar idonsa na zagi. Sai ga biri yana zaune a kan wani reshe yana ta faman cin duk abin da Kunkuru ya wahala ya noma. Tuni ya riga ya ci

dankalin Turawa mai yawa da kuma rabin gurji.

KUNKURU:

“Kai tsaya! Wannan kwandon da kayan da ke ciki nawa ne fa.”

BIRI:

“Ni wallahi ban san zancen da kake ba. Ni fa wannan kwandon tsintarsa na yi, an bar shi a bakin hanya.”

KUNKURU:

“To, ai na ajiye shi a nan saboda ƙishirwar da nake ji! Idan fa ba ka ba ni ba nan take, zan kai ƙararka wajen Giwa don ta yi mana shari’a.”

BIRI:

“Ai ni ban hana ka ba. Na fa san doka, domin kuwa cewa ta yi: Duk wanda ya ga wani abu a kan hanya, yana da damar ɗauka. Haka abin yake. Yanzu wannan kwando ya zama na wanda ya tsinta. Don kuwa idan ka tsinci abu ya zama naka.”

MAI BA DA LABARI:

Da Kunkuru ya ji wannan magana da Biri ya yi, sai ya yi shiru ya fara tunani. Don tsananin tunani har gumi ne ya fara zubo masa, saboda zafin da yake ji a cikin ƙoƙonsa. Yamma na yi sai ya tafi wurin Giwa. Kunkuru ya kwashe duk abin da ya faru ya shaida wa Giwa, kuma ya nemi ta yi masa hukunci na adalci. Da Malam-buɗa-mana-littafi da kuma ƙadangare su suka tsaya masa a matsayin shaidu, don kuwa a idonsu abin ya faru. Haka kuwa shi ma Biri ya halarci wannan wuri, sai dai kuma ya musanta duk abin da aka faɗa:

BIRI:

“In dai haka ne ai magana ta ƙare. Ni fa ganin wannan kwando na yi an bar shi a kan hanya. Da na ɗauke shi sai na riƙe. Kamar dai yadda

kuka sani ne, dokar dawa ta bayyana cewa, duk abin da mutum ya tsinta ya zama nasa. Idan ka tsinta ya zama naka. Don Allah, ranki ya daɗe Giwa, haka ne ko ba haka ba ne?"

GIWA:

"Idan dai gaskiya ake so, to lalle Biri yana da gaskiya. A haƙiƙanin yadda abin yake shi ne, duk abin da aka tsinta, to ya zama mallakin wanda ya tsince shi. Don haka kai Kunkuru sai ka yi haƙuri. Na san jidalin da ka sha kafin ka samu wannan amfani naka mai albarka, amma duk da haka dole a bar Biri ya tafi da wannan kwando da duk abin da ke cikinsa."

KUNKURU:

"Gaskiya, ba a yi mini adalci ba."

MAI BA DA LABARI:

Saboda tsananin takaici, Kunkuru kasa tashi ya yi daga wurin. Daga baya sai ya wattsake, har ma ya yanke shawarar ziyartar ƙanwarsa ko tana da 'yar totuwar da zai tsotsa ya samu ɗan dama-dama.
Don haka da gari ya waye sai ya kama hanya. Bayan ya yi ta tafiya ta ɗan wani lokaci a cikin tsananin zafin rana, sai kwatsam ya ci karo da Biri yana kwance a gefen hanya ya baje jelarsa, yana ta sharar barci, saboda cika cikinsa da ya yi da gurji da abarba da kuma dankalin Turawa.
Saboda wannan abu da ya gani, Kunkuru har kusan suma ya yi, daɗi kamar ya kashe shi. Ba tare da wani ɓata lokaci ba, sai ya ɗauki jelar Biri a bakinsa ya yi gaba.

KUNKURU:

"Yauwa! Yau kuwa sai na nuna maka yadda ake bin doka."

BIRI:

"Ku taimaka jama'a, ga ɓarawo, ku tare, ku tare! Me za ka yi da

jelata?"

MAI BA DA LABARI:

Shi dai Kunkuru bai amsa masa ba don kar jelar ta kuɓuce daga bakinsa. Can sai ga Mallam-buɗa-mana-littafi ya zo wucewa yana magana daga sama:

MALAM-BUƊA-MANA-LITTAFI:

"Anya kuwa Biri, ni fa gani nake Kunkuru tsintar jelarka ya yi a kan hanya, kuma ga dukkan alamu nema yake ya mayar da ita mallakinsa! Kuma ga Giwa nan ma mai shari'a da kanta."

GIWA:

"Gaskiyarka fa, Mallam-buɗa-mana-littafi! Ka ga Biri, idan kana jayayya sai ka kai ƙara kotu. Sai dai kuma ina jan hankalinka cewa wahalar banza kawai za ka yi. Domin kuwa a nan ma dokar daji tana aiki kamar yadda ta yi aiki a kan kwandon Kunkuru: duk wanda ya ga wani abu a kan hanya idan ya ɗauka ya zama nasa. Wato dai idan ka tsinci abu ya zama naka. Kai Kunkuru, abin da za ka yi kawai shi ne, sai ka yanke jelar biri, wataƙila ka dinga amfani da ita wajen korar ƙuda."

BIRI:

"Wayyo Allah! Jelata za a mayar izga? Don Allah ka yi haƙuri. Ka ga, ƙyale min jelata, ni kuma zan mayar maka da kwandonka da duk abin da yake ciki, har ma da ƙarin dankalin Turawa."

GIWA:

"Wannan bai isa ya fanshi jelarka ba. Idan dai ka yarda zan ba ka har zuwa gobe ka kawo min kwandon da ka faɗa da kuma ƙarin buhun dankalin Turawa da kuma buhun masara."

MAI BA DA LABARI:

Dole dai Biri ya yarda da wannan sharaɗi, duk kuwa da cewa ransa ya ɓaci. Daga nan sai Kunkuru ya sakar masa jelarsa yana murmushi. Kunkuru ya yi wa Giwa godiya kuma ya wuce gida abinsa yana mai gamsuwa da hukuncin da aka yanke. Yamma na yi sai Kunkuru ya haɗa abincinsa wanda ya ƙunshi dankali da gurji, kuma ya tsaya ya ci abincinsa bilhaƙƙi, saboda yadda ya ji daɗin irin adalcin da aka yi.

MAI GABATARWA:

Yanzu dai za mu iya cewa an yi maganin tsagerancin Biri, ko ba haka ba ne? Wannan ke nan na nuna mana cewar wani lokaci idan mutum na son ya zauna lafiya, to idan an yi masa kan kara, sai ya yi na itace. Sai dai a kula kar a cutar da wani garin ɗaukar fansa. To, wannan dai shi ne kyakkyawan sakamakon da Kunkurun nan mai ƙwazo ya samu.

Kuma laifin daɗi ƙarewa, domin kuwa wannan hikayar tamu ta "Biri da Kunkuru" ita ce ta ƙarshe a cikin jerin hikayoyi na ƙasashen Afirka waɗanda suke koyar da darussan zaman lafiya. Wanda ya rubuta waɗannan hikayoyin da kuka saurara baki ɗayansu shi ne Ibrahima Ndiaye, marubucin nan ɗan ƙasar Senegal. Kuna iya sake sauraron dukan waɗannan hikayoyi ta adreshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.

**’Yan wasa:**

Fatima Ado Gidan Dabino

Rabi Sufi

Abdullahi Garba

Mustapha Nasidi (Chuba)

Adamu Yusuf (Volunteer)

Awal yahya Abdu

Sadiq Mansur Murtala

Abdallah Sani shu’aibu

10.Aishatu Mohammed

11.Hadiza Jinta

12.Balarabe Sango II

Fatima Abdallah Kassim

Yusuf Lawal Gwazaye